Kada ku tsine masa, na rantse da Allah ban san wani abu daga gare shi ba sai dai yana son Allah da ManzonSa

Daga Umar Ibnul Khaɗɗab - Allah Ya yarda da shi -: Cewa wani mutum a zamanin Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - sunansa Abdullahi, kuma ya kasance ana yi masa laƙabi da jaki, ya kasance yana sa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - dariya, Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance ya yi masa bulala saboda giya, sai aka zo da shi wata rana sai ya sa aka yi masa bulala, sai wani mutum daga cikin mutanen ya ce: Ya Allah Ka tsine masa, ina mamakin yawan abin da ake zuwa da shi saboda shi?! sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya ce: "Kada ku tsine masa, na rantse da Allah ban san wani abu daga gare shi ba sai dai yana son Allah da ManzonSa".

[Ingantacce ne] [Bukhari ne ya rawaito shi]

A zamanin Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - akwai wani mutum sunansa Abdullahi, ana yi masa laƙabi da jaki, ya kasance yana sa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - dariya a cikin wasu daga cikin kalamansa, (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya kasance ya yi masa bulala saboda giya, sai wata rana aka zo da shi ya sha giya sai ya sa aka yi masa bulala. Sai wani daga cikin mahalarta ya zage shi, ya ce: Allah Ya tsine masa, ya mamakin yawan zuwan da ake yi da shi ya sha giya?! sai (Annabi) tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Kada ku yi masa mummunar addu'ar korewa daga rahamar Allah, na rantsae da Allah ban san wani abuba daga gare shi sai cewa shi yana son Allah da ManzonSa.

http://sunnah.global/hadeeth/ha/show/66214